[1]Bashir Rabi`u Abdullahi da [2]Zahraddeen Bala da [3]Idris Ashiru Shehu
[1da2]Hausa Department Federal University Dutsin-Ma Katsina State.
[3]College of Legal Studies Ringim.

# Adashi Jiya da Yau: Nazari a kan Sana`ar Adashi a Birnin Kano.

**Tsakure**

Wannan takrda ta yi bayani neakan yadda ake gudanar da sana`ar Adashi tsakanin al`ummar Hausawa, ytare da nuna wannan sana`a an jima ana yinta. Wannan takarda ta yi tsokaci ne akan wannan sana`a, musamman ta fuskar taimakon juna da nuna haɗinnkai tsakanin jama`a. Wannan takarda ta yi amfani da hanyoyin tattaunawa da mutane da suke da ruwa da tsaki a kan wannan sana`a. Haka muka wannn takarda an ɗora ta ne a kan ra`in adana al`ada (cultural sustaibability theory). A ƙarshe wannan takarda ta fito da sakamakon bincike kamar haka, wannan sana`a hanya ce ta taimakon juna tsakanin al`umma da kuma dogaro da kai. Sannan wannan bincike ya gano cewa wannan sana`a tana taimakawa wajen haɓakar tattalin arzikin al`umma amusamman a tsanin masu ta`ammali da ita. Haka kuma , wannan sana`a hanya ce ta adana tsohuwar al`ada da al`umma suka amfana da ita tun da daɗewa.

**Muhimman Kalmomi:** Al’ada da **Adashi da Sana’a.**
**Received**: 11/02/2025 Accepted: 20/02/2025 **GSM**:+234 8036793221
**Corresponding Author**: Bala, Z. **Email**: zbidris@fudutsinma.edu.ng
**Article Citation**: Bala, Z. da Abdullahi, B. R. da Shehu, A. (2025). **Adashi Jiya da Yau: Nazari a kanSana`ar Adashi a Birnin Kano.***Jalingo Journal of Languages and Literary Studies (JAJ0LLS). 9 (1) pp. 247-254.*
**Publishers**: Department of Languages and Linguistics, Taraba State University, Jalingo.
**ISSN**: 2488-9067

## 1.1 Gabatarwa

## 2.1 Ma`Anar Sana`a

An jima ana gudanar da nazarce –nazarce dangane da sana`o`in Hausawa na gargajiya. Da yawa an gudanar da su ne don bayyana yadda sana’o’in suke gudana da tarihinsu da kafuwarsu da kuma tarihin samuwarsu. Wannan takarda mai taken Nazarin a kan sana`ar adashi a birnin Kano za ta bi gwadaben wasu daga cikin irin waɗannan aikace-aikace inda za ta yi bibiyar hanyoyin da ake aiwatar da sana`ar adashi, musamman dangane da yadda yake taimkawa a tsakanin al`ummar Hausawa jiya da yau. Haka kuma wannan bincike zai gano tarihin samuwar sana`ar adashi a ƙasar Hausa da bayyana yadda ake gudanar da ita da kuma gudunmawar da take bayarwa wajen haɓaka tattalin azikin al`ummar Hausawa; musamman ta fuskar dogaro da kai da kuma haɓaka tattalin arzikin ƙasa. Binciken zai gudana ne a yankin birni da kewaye za a zaɓi wasu daga cikin ƙananan hukumomi domin gudanar da binciken a cikinsu. Kamar ƙaramar hukumar Dala, Fagge, Nassarawa da kuma ƙwaryar birni (munincipal). Wannan bincike zai yi bayanin yadda dashi yake a jiya da kuma yau. Sannan ya bayyana tasirin zamananci da ya samu sana`ar adashi. A ƙarshe binciken zai yi bayannin ciganab da masu sana`ar adashi sukesamuwajen buƙasar tattalin arzikin ƙasar Hausa da Hausawa bakiɗaya.

Kamusun Hausa (2006:387) ya bayyana sana`a da cewa “ sana`a tana nufin aikin da mutum yake yi domin samun abinci misali noma, wanzanci ko kuma aski”. Auta (2006:9) ya ce “ ta

hanyar aiwatar da sana`ar gargajiya ne Bahaushe yake biya wa kansa dukkan buƙatun da suka taso masa kuma yake warware matsalolinsa na yau da kullum". Aliyu (2024:182) sana`a ita ce hanyar saye da siyarwa da kuma sarrafa wanni abu zuwa ya zama wani nau`in daban ko domin musanyar kaya don mallakar abin da ba a iya samarwa kai sai an same shi daga wani". Ɗanmaigoro (2010:1134) cewa ya yi "sana`a aba ce da ta danganci wani abu na musamman wanda ya ƙunshi motsa baɓoɓin jiki domin samun abin biyan buƙatar rayuwa". Dan gane da waɗannan bayanai da suka gabata muke iya cewa " sana`a ta ƙunshi duk wani yunƙurin da ɗan`adam zai yi domin ƙoƙarin samun abin da zai rufawa kansa asirida shi daga ribar abin da ya samu ta hanyar yin ƙwadago ko kuma ta hanyar yin wata sana`a".

Maikwari, da Lawan, (2022) sun gudanar da bincike a kan sana`o`in mata. Binciken ya tabbatar da cewa mata sun tsunduma a cikin kasuwanci a ƙasar Hausa da ma wajen ƙasar Hausa, wasu ma sukan fita har ƙasashen waje domin yin kasuwanci da sauran sana`o`i.

Sani, da wasu (2019) sun gabtar da bincike mai taken wanda ya tuna bara.. biɗa da tanadi a tsakanin Hausawa matasa a yau. Wannan bincike ya yi ƙoƙarin bayyyana hanyar yin biɗa da tanadi a tsakani Hausawa a yau da kuma bamabance bambancen da ake iya samu a tsakanin kalmomin guda biyu. Sakamakon binciken ya nuna yadda aka samu koma baya dangane da riƙo da sana`0`i da kasuwanci tsakanin Hausawa. Haka kuma binciken ya gano rashin jari da rashin ilimin kasuwanci tsakanin matasa da yawan kaɓar bashi da masu sayen kaya suke yi. A ƙarshe binciken ya bayyana yadda al`adun biɗa da tanadi suka sami rauni tsakanin Hausawa. Wanda hakan zai zama babban miki ga tattalin arzikinsu.

**2.2 Taƙaitaccen Tarihin Samuwar Sana'ar Adashi**

Kalmar adashi ko dashi ana amfani da ita ne wajen bin hanyoyin tara kuɗi da nufin su taru domin biyan wata buƙata a rayuwa. Al`ummar Hausawa sun daɗe suna gabatar da harkokin da suka shafi tara kuɗi da inganta su domin samun biyan buƙatun rayuwa cikin sauƙi. Sannan tsawon lokaci Hausawa suka ɗauka suna gudanar da sana`ar adashi duk da cewa ba za a iya fayyace tun lokacin da aka fara ta ba, sai dai tarihi ya nuna cewa daga shekarar 1983-1985, sana`ar adashi ta bayyana ƙarara harma ta samu gidin zama. Haka kuma bayan wannan lokaci ta zauna daram.

**2.3 Abubuwan da Sana'ar Adashi take Buƙata**

Babu shakka kowacce sana`a na buƙatar samar da kayan gudanarwa waɗanda suke taimakawa ko sauƙaƙawa wajen ganin komai na wannan sana`a ya tafi yadda ake so. Irin waɗannan kaya sun haɗa da; Jaka, katin zuba kuɗi, littafin zubin adashi, asusun ajiya, amfani da rubutu da sauransu:-

**2.3.1 Jaka**

Masu aiwatar da adashi suna amfani da jaka domin taskace ko tsare ko kuma adana kuɗaɗen da suke karɓa a wajen jama`a. Wannan ya ƙunshi wanda suke karɓa ko kuma wanda yake buƙatar a bashi kuɗi (ajiya da karɓa).

**2.3.2 Katin Sa Hannu**

Katin sa hannu ana samar da shi ne domin buƙatar masu ajiye kuɗi ko karɓar kuɗin adashi, wanda ake tsarawa don amfanin masu ajiya. Irin wanna kati yana iya zama na musamman ne da sunan mai adashin ko kuma sunan kamfaninsa. Duk lokacin da aka karɓi kuɗi ana sa hannu a ciki wanda yake tabbatar da karɓar kuɗi a hannunn mai ajiya.

**2.3 3 Littafin Adashi**

Littafi ne da shi uban adashi yake amfani da shi na musamman domin shigar da adadin kudi da sunan duk waɗanda suke ajiya a wajensa da kuma adadin abin da suka ajiya koda yaushe.

**2.3.4 Jari**

Jari shi ne tsabar kuɗi ko kadara da duk mai sana`ar adashi ya kamata ya zama yana da shi domin kauce wa kowacce irin barazana da takan taso masa ko ta bayu ga wata asara.

**2.3.4 Asusun Ajiya na Banki**

Adashi abu ne da ya zo a zamanance yin amfani da asusun banki don ajiye kuɗaɗen jama`a a banki don gujewa asara ko sata ko annoba ko kuma wani abu da zai yi faɗo wa ba a shirya ba.

**2.3.5 Amfani da abin Rubutu**

Adashi abu ne da ya shafi lissafi don haka akwai buƙatar yin amfani da abin rubutu don nuna shigar kuɗi da fitar su. Haka kuma ana buƙatar yin amfani da biro don tantance sa hannun shigar kuɗi ko fitarsu rana da kuma lokaci.

**2.4 Abubuwan da mai Karɓar Dashi zai Keɓanta da Su**

**2.4.1. Amana:** dole ne maikarɓar kuɗin adashi ya kasance mai amana wanda aka sheda ko tabbatar da ingancin amanarsa wanda hakan ne zai ba jama`a nutsuwar ajiya a wajensa.

**2.4.2. Gaskiya :** gaskiya cika maki ne na amana duk mai maskiya zai kasance mai amana, domin gaskiyar ita ce za ta tallata hajarsa a wajen al`umma. Sannan za ta shiryar da shi ga barin cin kuɗin mutane.

**2.4.3. Haƙuri:** dole ne mai dashi ya siffatu da haƙuri, domin kasancewarsa mai hulɗa da mutane mabambanta, wani ya ɓata masa wani kuma ya munana masa amma idan yana da haƙuri hakan zai ƙara masa ƙaimi wajen kula da sana`arsa.

**2.4.4. Mai dakiyar zuciya:** dole ne ya siffantu da dakiyar zuciya domin kuɗaɗen al`umma za su dinga shiga hannunsa ga kuma buƙatun rayuwa idan ba zuciya dakakkiya sai ya ɗauki kudin mutane ya biya buƙatarsa da su, aɗarshe a yi ta rikici tsakaninsa da jama`a.

**2.5 Ire-Iren Adashi**

Adashi ya kasu kashi daban-daban ya danganta da ɗarfi ko nau`in sana`ar da mutum yake yi. Kaɗan daga ciki sun haɗa da :-

| | | |
|---|---|---|
| i. Dashin ma`aikata | iɓ. Dashin leburori | ɓii. Dashin Gata |
| ii. Dashin `Yan kasuwa | ɓ. Dashin Ɗalibai | ɓiii. Dashin tari |
| iii. Dashin matan aure | ɓi. Dashin azumi | iɗ. Dashin watanda |

Duk waɗannan ire-iren dashi ne da jama`a suke amfani da su domin samun nasarar rayuwa da kuma cimma muradin da ake nufi.

2.6 **Sharhin Ayyukan Magabata**

Abu-Ubaida da Umar da Ibrahim (2019, sh. 44-50) aikin nasu ya mayar da hankali ne kan tasirin biɗa (nema) da tanadi (tattali) ga cigaban tattalin arziƙin Bahaushe. Takardar ta yi bitar ma'anoni da kamanci da kuma wasu bambance-bambancen da ake iya samu tsakanin kalmomin guda biyu. Bayan haka, an nazarci yadda lamarin ya ke ga Bahaushen yau. Bugu da ƙari, an yi bitar gurbin biɗa da tanadi ga bunƙasar tattalin arzikin Bahaushe. Domin binciken ya kuɓuta daga jin kunyar ilimi da masu ilimi, an bi manyan hanyoyi bincike guda biyu waɗanda da su ne aka yi amfani wajen tattara bayanai yayin binciken. Hanyoyin su ne, bitar ayyukan da suka gabata da kuma tambayoyi. An ɗora aikin kan tunanin Bahaushe na ***"Mai nema na tare da samu."*** Binciken ya gano cewa, biɗa da tanadi ba a matsayin tasiri kawai suka kasance ba, su ne ke tallafe da tattalin arzikin Bahaushe a tarihance. A ɓangare guda kuma, tasirin zamani da sauye-sauyen yanayi ya kawo sauyi ga yadda tsarin yake a baya. Hakan kuwa ya samar da giɓi bayyananne ga tattalin arziƙin Hausawa, duk kuwa da cigaban da aka samu a ɓangare guda. A bisa haka ne takardar ke ba da shawarar cewa, a yi hoɓɓasar nazartar hanyoyin ɗinke wannan ɓaraka a matakin ɗaiɗaikun al'umma da gundumomi da kuma a gwamnatance.

**3.1 Hanyoyin Gudanar da Bincike**

Wannan ɓangare zai yi bayani hanyoyin tattara bayanan da aka yi amfani da su a wannan bincike. Kamar kowane bincike da aka gabatar shima wannan akwai wasu matakai na samun bayanai kamar haka:

**3.1 Tambayoyi** domin samun waɗansu bayanai da aka neman saninsu daga bakin masu yin wannan sana`a da abokan hulɗarsu haɗi da masana da manazarta domin samun ƙarin haske.
**3.2 Lura:** an sa ido domin lura da wasu al`amura domin ƙara fahimtar yadda ake gudanar da ita wannan sana`a ta dashi.
**3.3. Nazarce-nazarce:** wannan takarda an yiƙoƙarin bibiyar ɗakunan karatu domin duba da duk wani abu da yake da alaƙa da wannan sana`a da kuma wasu sana`o`in Hausawa na gargajiya.
**3.4. Tattaunawa:** an samu damar tattaunawa da rukunin mutane waɗanda suka haɗa da mata da maza manya da matsa, ma`aikata da `yankasuwa, leburori da kuma masu ruwa da tsaki a kan harkar adashi da sauransu. Sannan za a samu damar zaɓar wasu daga cikin masu daga cikin iyayen adashin da kuma waɗanda suke zuba kuɗi a harkar adashin.

**4.1Yadda ake Gudanar da Sana'ar Adashi**

Ana gudanar da adashi ne idan mutane sukan aminta da wani ko wata wanda zai zama abinda ake kira Uban dashi ko Uwar dashi wadda za su dinga zuba kuɗi a wajensa/ta har zuwa wani lokaci, domin cimma wata buƙata. Haka kuma, za a iya tara kuɗi da nufin cimma wata buƙata da ta taso zuwa wani lokaci a raba kowa ya biya buƙatarsa.
Wani lokaci, mutun ne da kansa yake tsara wa kansa yin wani dashi ta hanyar tuntuɓar wasu domin su haɗa ƙarfi waje ɗaya da nufin cimma wata buƙata. Irin wannan za a zaɓi wanda zai zama uban dashi domin ya dinga tara kuɗin a wajensa.
Bugu da ƙari, wani salon daban mai yin dashi shi kaɗai ko ko ƙarƙashin kulawar wani ko wata kan yi amfani da bankin ƙasa ko gwangwani sai a yi mukulli a rufe a cigaba da zuba kuɗi har sai lokacin da aka amince a buɗe kowa ya ɗauki kasonsa. Irin wannan ana la`akari da zubin da kowa yake yi ta hanyar lissafin abinda ya zuba a kullum har ƙarshen lokacin da aka buɗe.

**4.1.1 Yadda ake Gudanar da Sana`ar Adashi a Jiya**

Duba da yanayi da kuma ɗaukar adashi a matsayin hanyar tara kuɗi tsakanin al`umma, ya sa mutane suka ga dacewar yin wannan harka a matssayin sana`a. A dashi a jiya ya ginu ne bayan taruwar mutane wanda suka ƙunshi abokai ko ƙawaye ko `yan`uwa waje ɗaya da nufin tara kuɗi don cimma wata muhimmiyar buƙata bisa wata yarjejeniya ko ƙa`ida.
Irin wannan adashi ana yinsa ne bisa tsarin na gargajiya wanda ya ginu tun iyaye da kakanni, wanda yake gudana a lokacin da al`umma suka ga damar tsarawa. A wannan lokaci akan tsara cewa kowa zai kawo kuɗi ne a dinga zubawa har sai har sai abinda ya cika asusu ko bankin sannan a fasa a bawa kowa rabonsa. Haka kuma, ana iya tsara adashi domin fuskantar wata hidima kamar aure ko suna ko maulidi ko sallah sai a ƙirƙiri dashi da zai isa biayn wannan buƙata.
Baya ga haka, wani ko wata kan tafi kasuwa ya siyo asusu domin ya ajiye a wajensa ko wajen wani, ya yi ta zuba kuɗi har sai ranar da ya ji wata buƙata sannan ya fasa domin magance ta. Idan kuwa a cikin yama ne uban dashi ko uwar dashi kan tuntuɓi masu ra`ayi domin fara dashi. Sannan za a iyakance yawan kuɗin da za a dinga zuba wa kullum.

**4.1.2 Kayan Aikin Sana'ar Dashi a Jiya**

Akwai muhimman abubuwan da ake amfani da su a matsayin kayan sana`ar adashi a jiya. Waɗanda suka haɗa da:-

a.Banki e. Sanayya
b. Jaka f. Karan dashi
c. Kadara g. Kuɗi
d. Ɗan aike

### 4.2. Yadda ake Gudanar da Sana'ar Dashi a Yau

Gudanar da sana`ar dashi a yau ya saɓa ko ya sha bamban da yadda ake gudanar da shi a jiya. Wannan kuwa ya faru ne sakamakon cigaban zamani da kuma sauyin yanayi da bunƙasar al`umma.

Adashin zamani ana yin sana`a ne ta hanyar tsarawa da lissafawa, da kuma lissafa abinda mutum zai ɗauka tun kafin a soma ko ƙare dashin, tare da kafa dokoki da sharuɗɗa wani lokaci har da samar da yarjejeniya saboda samun saɓani idan mutum ya karya ƙa`ida ga sakamakonsa.

Masu gudanar da dashi a yau, sun zaɓi su yi amfanni da katin zubi ko kuma sa hannu wanda aka tsara shi layi-layi tare da rubuta sunayen iya adadin masu zubin dashin na gabaɗaya ko kuma na ɗai-dai ku ne, sannan ana siyan kati a gurin mai adashi. Duk san da mutum ya zuba za a rubuta masa iya abinda ya zuba ko ya bayar. A wani lokaci mai gabatar dashi yana da littafi na musamman don rubuta duk abinda ya shigo na kuɗin zubin dashin al`umma wannan hanya ce ta adana bayanansa.waɗanda suka bashi kuɗi yana karɓa ya shigar.

Duk lokacin da mutum ya zo karɓa sai a lissafa rubutun adadin kuɗin da aka rubuta wanda yake wajensa da wanda yake wajen mai adashi domin kaucewa son rai ko matsala.

Haka kuma, a wannan zamani ana gudanar da adashi ta hanyar turawa a wayar hannu, tare da tura shaidar tura kuɗi ga uban dashi. Ana gabatar da ƙuri`a ko zaɓar ɗaukar da mutum yake so a bashi, sannan akan lura da yanayin mutum ko kasuwa ko aiki wajen bashi ɗaukar farko, ko wata buƙata da ta taso masa domin magancewa. Sannan duk wanda ya yadda katinsa sai an yi ƙwaƙƙwaran bincike domin tabbatar da abinda ya zuba kafin a sallame shi.

#### 4.2.1. Kayan Aikin Sana'ar Dashi a Yau

Zamani rigar ƙaya, domin a wannan lokaci an samu yawaitar hanyoyin gudanar da sana`ar adashi yanayi da lokaci ya haifar da su waɗanda suka haɗa da:-

a. Katin dashi b. Asusun banki c. Kuɗi d. Littafin karɓar kuɗi e. Abin rubutu f. Ilimi g. Karan dashi

### 4.3 Nagartar masu Sana'ar Dashi

Masu sana`ar dashi mutane ne waɗanda bisa al`ada al`umma suka aminta da su ta fuskar gaskiya da riƙon amana da kaƙuri sannan da son zaman lafiya. Wannan halaye sune suka bawa jama`a dama domin ɗora musu nauyin ajiyar dukiyarsu ta hanyar adashi.

Ko da zamani ya riski wannan sana`a sai ya zamana maimakon mutum ya jira a zaɓe shi a ɗora masa nauyin aiwatar da adashi sai ya zama duk lokacin da da kyawawan halayensa da gaskiyarsa da amana, sai ya tallafawa al`umma zai fara ko soma yin adashi wanda duk ya san shi da irin wannan ɗabi`a sai ya yi rigista a wajensa.

Da zarar mutane sun sami labarin sai su hanzarta wajensa kada dama ta kuɓuce musu. Sannan kuma dole ne mai yin wannan sana`ar ta adashi ya zama mai taka tsantsan domin gudun cin dukiyar al`umma. Sannan ya zama mai mutunci mai haƙuri da halin rayuwa da na jama`ar da yake hulɗa da su. Lallai ne masu yin wannan sana`a su zama suna da tsoron Allah matuƙa ta yadda za su tsarewa al`umma dukiyarsu tare da rubutawa kowa abinda ya bayar a katinsa.

### 4.4. Yadda mai Adashi yake Samun Kuɗin Shiga

Ma`abota wannan sana`a ta adashi na samun kuɗin shiga ta hanyoyi da dama daga ciki akwai;-

i. Karan dashi ii. Katin dashi iii. Juya kuɗaɗe

### 4.5 Yadda Adashi yake Bunƙasa Tatalinarzikin Kasa

Babu shakka adashi ya zama wata hanya wadda ake bi domin samunn ƙarin ci gaba a rayuwa. Akwai abubuwa masu yawa waɗanda yin adashi ya sa ya zama dalili ko kuma asali ko tafarkin bunƙasa arziki mafiya yawan wasu mutane daga cikin ɗinbin al`ummar Hausawa

i. Samar da jari, da yawa daga cikin mutane sun samu damar mallakar jari ne daga adashi, wannan kuwa ya faru ne saboda mai da hankali da suka yi wajen tara kuɗi ta hanyar adashi. Da yawa mutane sun tsaya da ƙafafunsu a harkar kasuwanci ko sana`o`i.

ii. Mahalli, mallakar muhalli wata babbar dama ce a rayuwa, akwai ɗinbin al`umma da suka mallaki muhallin ta hanyar adashi. Daga ciki akwai ma`aikata waɗanda ake cira daga albashinsu domin su mallaki fili, wasu kuma `yankasuwa ne suke zubi lokaci-lokaci kuma sun mallaki muhalli ta wannan hanyar.

iii. Aure, amfanin adashi bai tsaya a nan ba, mutane da dama ta hanyar adashi suke samun damar yin aure; saboda kuɗi suna wahalar taruwa a wajen wasu saboda haka suna buƙatar adashi domin samun damar tarawa da mallakar abubuwaa rayuwa.

iv. Hana almubazzaranci. Wasu mutane suna yin amfani da adashi ne domin ya rage musu kashe kuɗi bai gaira ba dalili. Yin adashi zai taimaka musu wajen ajiye kuɗi da mallakar wata kadara da za ta amfani rayuwa.

v. Rufin asiri. Adashi hanya ce da take taiamakwa al`umma wajen samun rufin asirin rayuwa. Domin kuwa irin wannan hali yakan taimaki rayuwarsu wajen saita ta da hawa kan tsari mai inganci.

vi. Dogaro da kai. Matuƙar mutum yana yin adashi zai bashi damar dogaro da kansa, domin duk lokacin da ya ɗauki nasa kason zai yi wani abu da zai inganta rayuwarsa da shi.

vii. Haɗin kai. Masu yin adashi sukan samu fahintar juna da haɗin kai a tsakaninsu, musamman a tsakanin ma`aikata da `yan kasuwa. Domin ana samun alaƙa ta ban gishiri in baka manda a tsakanisu. `yan kasuwa sukan kawo kaya ga ma`aikata domin samun sauƙin tafiyar da rayuwa. Sannan a dinga biyansu kuɗin a hankali.

## 5.1 Sakamakon Bincike

Wannan takarda mai taken adashi a kasar Hausa ta yi nazarin yadda ake gudanar da sana`ar adashi a jahar kano, musannan a cikin birni da kuma hanyoyin da ake bi wajen gudanar da wannan sana`a a jiya da yau. Wannan bincike ya gano yadda zamananci ya yi tasiri a cikin wannan sana`a musamman wajen yin amfani da kafefen sadarwa na zamani a cikin wannan sana`a. Haka kuma wannan bincike ya gano yadda sanan`ar adashi ta zama hantsi leƙa gidan kowa da wuya ka binciki gida baka samu mai yin adashi ba. Binciken ya tabbatar da cewa adashi yana taimakawa al`ummanr Hausawa wajen hana ɓarna da kashe kuɗi, sannan ya koya wa al`ummar Hausawa tattali da yiwa kai hidima.

## 5.2 Kammalawa

Wannan takarda ta yi bayani game da yadda ake aiwatar da sana`ar adashi a wasu daga cikin ƙananan hukumomin birni da kewaye da ke jahar Kano. Wannan takarda ta kawo taƙaitaccen tarihin sana`a daga bakin masana sannan kuma an gano adashi yana da mutuƙar muhimmanci a gurin Hausawa musamman ga ƙananan `yakasuwa da masu ƙananan sana`o`i da duk wani mai ƙaramin ƙarfi da neman jari dashi yana taimaka masa wajen bunƙasar kowanne aiki. Wannan ya sa adashi ya zamo ɗaya daga cikin hanyoyin tallafwa rayuwar mutane matsakaita ta fuskar rage nauyin ɗawainiyarsu ta hanyar adashi. Haka an tabbatar da ceawar adashi hanya ce ta gano zaƙaƙuran mutane masu amana da kuma bambance wa da baragurinsu wajen rashin iya riƙe amana.binciken ya gano matsalolin adashi sun haɗa da ƙin zubi lokacin da yakamata a yi ko kuma karɓar kuɗin mutane a gudu wannan duk ana samu a cikin wasu maha`intan mutane.

## Manazarta

Abu-Ubaida, S.; Umar; B. da Ibrahim, M. (20190. Wanda ya Tuna Bara...: Biɗa da Tanadi a Tsakanin Hausawa Matasa a Yau. *Global Academic Journal of Humanities and Social Sciences, 2019; 1(2) 44-50 DOI: 10.36348/gajhss. 2019.v01i02.001 Available online at http: / /gajrc.com/ ISSN: 2706-901X (P) ISSN: 2707-2576 (O).*

Aliyu, B.S. (2024). Sana`ar Wananci a Kasar Hausa: *Gudunmawar da take Bayarwa da ƙalubalen da take fuskanta wajen bunƙasar Tattalin Arzikin Kasa a Karni na 21 FUDJOHAS. Vol. 1 No. 3 PP.*

Auta, A. L. (2006). Tattalin Arzikin Al`umma. Nazarin Sana`o`i da Kasuwancin Hausawa. *A cikin Algaita Journal of Current Resaeerch in Hausa Studies. Vol. 1 No. 4 PP*

CNHN. (2006). Kamusun Hausa. Na Jami`ar Bayero. Ahmadu Bello University, Zaria. Ɗanmaigoro, A. (2010). *Sana`o`in Hausawa da Fulani.* A cikin Al`ada da Ɗabi`un Hausawa. Kaduna El-Abbas Printing and Media Concept.

Maikwari, H.U. & Lawan, M.S. (2022). Gudubmawar Matan Hausawa Wajen Bunƙasa. Tattalin Arzikin Kasar Hausa. *Conference Proceedings on Women and their contribution to Hausa society. PP.229-238*

Sani, A. Da wasu (2019). Wanda ya Tuna bara...Bixa Da Tanadi A Tsakanin Hausawa Jiyada Yau. Global Academic Journal of Humanities and Social ScienceNo.1 (2). PP. 44-50.

**Mutanen da aka Tattauna da su**

| | | | |
|---|---|---|---|
| Alhaji Saminu Mai adashi | Litinin | 24/6/2024 | Dala |
| Mal. Halima Hamisu | Talata | 9/7/2024 | Dala |
| Mal. Jummai Ibrahim | Laraba | 10/7/2024 | Dala |
| Mal. Rabi`u Tava kaxan | Lahadi | 30/6/2024 | Munincipal |
| Mal Kamilu Sagagi | Alhamis | 4/7/2024 | Munincipal |
| Mal. Jibril Shu`aibu | Laraba | 10/7/2024 | Munincipal |
| Mal. Aminu Mai adashi | Litinin | 15/7/2024 | Fagge |
| Mal. Salisu Babban giji | Alhamis | 13/6/2024 | Fagge |
| Haj. Talatu Rabi`u | Asabar | 15/6/2024 | Fagge |
| Mal. Iliyasu Rabi`u | Asabar | 6/7/2024 | Nassarawa |
| Mal Mukhtar Muhammad | Asabar | 15/6/2024 | Nassarawa |
| Haj. Marwa Mukhtar | Litinin | 17/6/2024 | Nassarawa |